## EPISODE 24

**<u>Characters</u>**
*Alhaji Bature*

*Laraba*

*Dr. Daoud*

*Hannah*

*Kande*

*Mai-Unguwar*

---

**Scene 1**
**Northern Kaduna, Community Health Centre.**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |
| 2. | **SFX:** | **<u>SOUND OF SHUFFLING PAPERS.</u>** |
| 3. | **ALH. BATURE:** | So Doctor Daoud, don Allah kar ka barni cikin tunani, ka gaya mun sakamakon gwajin. Wanene uban yaran, ka gaya mun mana! |
| 4. | **DR. DAOUD:** | Ina zuwa kan wannan Alhaji. Ina son na san ko ka gaya wa matarka ta farko. |
| *5.* | **ALH. BATURE:** | **(IRRITATED)** Likita, ta yaya zan yi irin wannan magana tare da Hindatu? Ta yaya? Ko da nayi ma, ba zata yarda ba. Saboda haka babu ma amfani. |
| *6.* | **DR. DAOUD:** | Ko ma menene zata yi, ya kamata ka gaya mata. Babu yadda zaka cire ta daga maganar bayan ya shafe ta. |
| 7. | **ALH. BATURE:** | **(IMPATIENTLY)** Likita don Allah menene sakamakon gwajin, ka gaya mun kawai. Ba zan iya jurewa ba kuma. |
| 8. | **DR. DAOUD:** | **(CLEARS THROAT)** Toh Alhaji, gwajin ya nuna cewa kai ne uban yaran nan guda 3. |
| 9. | **ALH. BATURE:** | **(EXCITED, CONFUSED)** Me?! ‘Yan matan nan guda uku ‘ya’ya na ne? Abun da kake gaya mun kenan? |

10. **DR. DAOUD:** Eh, kaine uban su Alhaji Bature.

11. **ALH. BATURE:** **(CONFUSED)** Amma ta yaya ne? Wato, ta yaya za'a ce mini wai ba zan iya haihuwa ba yanzu bayan na haife yara can baya?

12. **DR. DAOUD:** Komai na iya faruwa Alhaji. Abun da ya faru da kai shine ake kira '*Secondary Infertility*' a turance.

13. **ALH. BATURE:** **(UNCERTAIN)** Likita, *secondary infertility* kuma*?* Wannan na da magani ko kuma wata taimako?

14. **DR. DAOUD:** Eh, akwai abun da za'a iya yi. Ka gani, zan rubuta maka takarda domin kaje kaga wani likita a babban asibiti. Shi zai taimaka wajen baka shawara da maganin da kake bu*k*ata.

15. **SFX:** **SOUND OF RUSTLING PAPERS.**

16. **DR. DAOUD:** Don Allah Alhaji Bature, idan zaka je kaje tare da matanka domin a baku takaitaccen shawara gabaki *d*ayanku.

17. **ALH. BATURE:** Toh, Dr. Daoud. Nagode da wannan albishrin. Don Allah ka gaya mun wanene zan gani a babban asibitin.

18. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Scene 2**

*Northern Kaduna. Kande's House. Late Afternoon.*

19. **SFX:** **SOUND OF SITTING ROOM AMBIENCE. RADIO PLAYING IN THE BACKGROUND**

20. **LARABA:** **(SCOLDING)** *Haba* Hannah! Ki kalli yadda kika zama. Me yasa baki kula da kanki? Rai guda kike dashi fa.

21. **HANNAH:** Laraba in iya *kok*ari na, abun na yi mun wuya ne. Musamman da nake jin ba*k*in ciki.

22. **LARABA:** Hannah ya kamata ki daure. Ki *k*ara *kok*artawa. Bai kamata ki shiga cikin irin wannan yanayi a yanzu ba.

23. **HANNAH:** Kin san cewa kwanan nan ina mantawa na ci abinci? Na ma fi mantawa na ci abinci akan na tuna na sha *k*wayoyin tazzaran haihuwan da nake sha.

24. **LARABA:** Ke fa! Kina tuna min da mutane dayawa dake tamabaya na akan yadda zasu iya shan *k*wayoyin tazzaran haihuwa akai-akai. Suna cewa wai sun cika mantawa.

25. **HANNAH:** Me kike gaya musu?

26. **LARABA:** Toh, ina yawan gaya musu cewa sai sun ha*d*a da tattaunawa tare da mazajensu. Ta wannan hanya ne zasu fahimci junansu akan hanyar tazzaran da zai dace musu.

27. **HANNAH:** **(SOFT SOBS)** Wannan shawara ce mai inganci Laraba.

28. **LARABA:** Ahn ahn Hannah. Me yasa kike kuka kuma?

29. **HANNAH:** **(STILL SOBBING)** Babu komai. Na tuna ne da yadda Danjuma ya raka ni lokacin da zan je asibiti domin samun shawara akan tazzaran haihuwa, da kuma yadda yake saka mun sanarwa a waya ta domin kar na manta na sha *k*wayoyin.

30. **LARABA:** Eyyah! Ki daina kuka Hannah. Don Allah kiyi ha*k*uri. Kiyi tunanin cikin da kike *d*auke dashi. Yauwa, kin yi magana da Danjuma?

31. **HANNAH:** **(ANGRY)** Don me, eh Laraba? Don me? Domin nayi mishi albishir da auren Tina da zai yi ko?

32. **LARABA:** **(SYMPATHETIC)** Haba Hannah! Kiyi ha*k*uri. Kin ga, ya kamata ki saurare shi. Gefen Tina ne kawai kika ji fa.

33. **HANNAH:** **(BITTERLY)** Bana bu*k*atar shi. Bana ma son naji muryarshi. Abun ta*k*aici shine wai budurwarshi Tina tana ta amfani da lambobi kala-kala ta kira ni ta tsogale ne.

34. **LARABA:** **(SHOCKED)** Me?! Kin tabbata cewa Tina ce? Ta yaya ta samu damar tayi miki wannan? Ban yarda ba.

35. **HANNAH:** **(UPSET, CLOSE TO TEARS)** Kin gani ba? Dama na san kema baza ki yarda ba. Abun da haushi, babu mai yarda dani idan na gaya musu abun da Tina take yi mini. Ba’a barta a baya ba fa.

36. **LARABA:** Ba haka bane Hannah. Abun ne yake ta da*d*a daburcewa, yana rikicewa. Kin san na ta*b*a ha*d*uwa da Tina a gidanki. Tayi mun kama da mai kirki da hankali. Ba wanda zata iya aikata wannan abun ba.

37. **HANNAH:** **(SOFT CRY)** Na san ba za ki yarda dani ba.

38. **LARABA:** Na yarda dake mana Hannah. Abun na bani mamaki ne kawai, wai ace mutum na iya yin irin wannan muguntan.

39. **HANNAH:** Ah Laraba! Shedaniya ce fa. Duk kirkin da take yi munafurci ne kawai, don ta samu ta cika burinta. Ai yanzu ta malleke shi. Ta mallaki Danjuma. **(CRYING)** Kuma bayan ta samu ta kar*b*e shi ba zata *k*yale ni ba.

40. **LARABA:** **(SYMPATHETIC)** Kin ga Hannah, bari na baki shawara, idan ta sake kiranki ki kwashe maganar a cikin wayarki. Ta hanyar ne kawai zaki iya fallasa nufinta. Ki samu sheda. Danjuma ya ga wace irin mata ce ita.

41. **HANNAH:** **(RELIEVED, SNIFFING)** Kin san menene? Abun da zan yi kenan kuwa.

42. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Scene 3**

**Northern Kaduna. Mai-Unguwa's House. Evening.**

43. **SFX:** **<u>SOUNDS OF ROAD AMBIENCE.</u>**

44. **MAI-UNGUWA:** Me*?!* Bature ka tabbata da abun da kake fa*d*i?

45. **ALHAJI:** Eh Mai-Unguwa, na tabbata. Gwajin da nuna cewa nine uban duk 'yaya na guda 3.

*46.* **MAI-UNGUWA:** Alhamdulillah*!* Yanzu zaka samu kwanciyar hankali. Ni tuntuni na san cewa yaranka ne.

47. **ALHAJI:** Na yarda da kai. Kuma na san Hindatu mata ce mai kirki da mutunci. Na ru*d*e ne kawai har na kasa tunani me kyau. Komai ya taso mun ne ba tsammani.

48. **MAI-UNGUWA:** Hmm, yanzu sai ka kyautata mata Alhaji Bature. Ka bata hakuri, ka saka ta cikin ba*k*in ciki sosai.

49. **ALHAJI:** Eh, abun da zan yi kenan Mai-Unguwa.

50. **MAI-UNGUWA:** Allah Sarki Hindatu! Mata ta kawarta ta gaya mun cewa bata daina kuka ba, kuma ta *k*i ta ci abinci. Ina tausaya mata sosai. Mun gode

wa Allah cewa gwajin ya fitar da ita. Bature sai fa ka bata ha*k*uri ka nemi gafaranta.

51. **ALHAJI:** **(REMORSEFUL)** Toh, zan yi hakan, nayi al*k*awari. Naji kunya sosai wallahi. Baza ka iya gane irin rikicin da wannan al'amarin ya kawo a gida na ba, wa yara na da dai kowa-da-kowa. Abun dai ba'a cewa komai.

52. **MAI-UNGUWA:** Kama gode wa Allah cewa kana da mata masu kirki. Kalli yadda Safiya ta kula da gidan da yaran tunda Hindatu ta shiga halin ba*k*in ciki.

53. **ALHAJI:** **(AGREES)** Eh wallahi. Na gode wa Allah ma komai. Wannan al'amarin ya bu*d*e mini idanuwa game da abubuwa dayawa. Yanzu na san cewa iyali na nada matu*k*ar ha*d*in kai.

54. **MAI-UNGUWA:** **(AGREES)** Gaskiya! Amma dai sai na nanata maka kaje ka ba Hindatu ha*k*uri. Ta sha wuya sosai. Kana bu*k*atar gafarar ta.

55. **ALHAJI:** Na *d*au al*k*awari zan bata ha*k*uri. Zan yi.

56. **MAI-UNGUWA:** Toh. Ina wata bu*k*ata kuma daga gare ka Bature

57. **ALHAJI:** Ah Mai-Unguwa, naji da*d*i yau fa, ko menene ka tambaya zan yi maka.

58. **MAI-UNGUWA:** Bature, wani abu dake faruwa a wannan garin ya jawo hankali na**.**

59. **ALHAJI:** Ah menene Mai Unguwa?

60. **MAI UNGUWA:** Wannan sa hannunka cikin janyo gaba tsakanin Hassan da Husseini bai da kyau.

61. **ALHAJI:** Toh Mai Unguwa.

62. **MAI UNGUWA:** Ka san ana *d*aukan ka mutunci a cikin gari, saboda haka sai kayi da hankali kana kulawa Bature.

63. **ALHAJI:** Mai-Unguwa naji ka.

64. **MAI UNGUWA:** Don Allah, ka bar maganar za*b*en Hassan. Ka daina cin zalin *d*an-uwansa Husseini saboda maganar eh? Hakan bai da kyau.

65. **ALHAJI:** Toh Mai-Unguwa, na ji.

66. **MAI-UNGUWAR:** Don Allah kar ka sake sa hannu a cikin maganar. Ka bar mutane su za*b*i wanda suke so, kaji ko?

67. **ALHAJI:** Mai-Unguwa, aboki na, kullun dai kana da gaskiya. Zan yi yadda ka shawarce ni.

68. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Scene 4**

*Northern Kaduna. Kande's House. Night***.**

69. **SFX:** **SOUND OF ROOM AMBIENCE. CREAKING SOUND OF A CEILING FAN**

70. **HANNAH:** **(PERSISTANT)** Mama na gaya miki ki daina yi mini maganar Danjuma. Bana son naji sunarsa, don Allah Mama.

71. **KANDE:** Subhanallah! Hannah! Kin haukace ne? maigidanki ne fa muke magana ba wani ba*k*o ba. Yayi ta kiran wayar ki amma kina *k*in ki kula shi. Me kuma kike son yayi?

72. **HANNAH:** Mama menene mutumin da yake da ikon ya ci amanar aurenmu, akan gadonmu zai gaya mini? Me kuma? Ai ya gama komai.

73. **KANDE:** Hannah, ki kwantar da hankalinki. Kina son ki cigaba da zama haka ne? kar ki manta cewa kina dau*k*e da cikin Danjuma, kuma zai fi idan kin san abun da zaki yi kafin ki haihu.

74. **HANNAH:** Mama, kar ki dame kanki game da wannan. Ba zan gaya wan Danjuma komai ba game da maganar cikin nan, sai ya yarda ya amsa laifinsa.

75. **KANDE:** Ta yaya kike tsammanin mutum zai amsa laifin da bai sani ba? Kuma ma Tina ta ce wai babu abun dake tsakaninta da shi, haka ma shi Danjuma ya fa*d*a. Menene kike son ki ji kuma?

76. **HANNAH:** Ina son su fa*d*i gaskiya. Ban damu da abun da Tina ta ce ko tayi ba. It shai*d*aniya ce. Shi kuma Danjuma, idan ya cigaba da *k*arya kamar yadda Tina take yi, shi ya sani!

77. **KANDE:** **(SMILING)** Hannah, ni mahaifiyarki ce kuma kin san ba zan yi miki *k*arya ko na ru*d*e ki ba. Nayi magana tare da Danjuma tun ranar nan kuma ya tabbatar mini bai san komai akan abun ba.

78. **HANNAH:** **(GRUMBLES)** Dole ai ya musanta.

79. **KANDE:** Ya kamata ki gan shi, duk ya bi ya rame ya lalace. Danjuma na iyakan kokarinsa ya dawo da ke. Me yasa baza kiyi haka ba kema Hannah?

80. **HANNAH:** Domin ni ba wawiya bace da zan yarda da *k*aryarsa da yaudararsa. Yanzu ma ina da shaidan duk ala*k*ar da yake *b*oyewa tsakaninsa da Tina.

81. **KANDE:** Kin tabbata? Menene shaidan? Daga ina kika samo shaidar?

82. **HANNAH:** **(SMILING)** Maganarsu ne a waya tare da Tina. Ki ji abun da tace mini…

83. **SFX:** **<u>SOUND OF PHONE CONVERSATION BEING PLAYED, AS TINA'S VOICE IS HEARD WITH PHONE EFFECTS REPEATING THESE TWO LINES (EPISODE 18 LINE 107, AND EPISODE 23, LINE 9)</u>**

84. **KANDE:** **(SHOCKED)** Amma Hannah! Wannan fa Tina ce. Menene nake ji haka??? Wannan yarinyar ta bani mamaki, ashe muguwa ce! **(SNAPS FINGERS)** Ehhhhh??? Toh ai zamu gani!

85. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**